


# Jama'a da Al'adunsu

Littafin karatu a sauƙaƙe - Mataki na 4

Hausa

Zuwa ga malamai da iyaye:

Kafin a fara amfani da wannan tsarin koyon karatu, dole sai ɗalibi ya: • San amon sautukan haruffan Hausa; • Iya gane kalmomin da aka saba da su.

Jama'a da Al'adunsu

Hausa Nigeria

Copyright © 2017, Enabling Writers Project - American University of Nigeria

http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/
http://creativecommons.org/licenses/by/4.0/ An yarda ka yi amfani da wannan aikin ta wajen harkar kasuwanci. Kana iya ɗaukar aikin nan a yadda ya ke ko ka yi ƙari akai. Dole ne ka ajiye haƙƙin mallaka da kuma alaƙanta aiki ga marubuta, masu zayyana da sauran su. ISBN

Grace Malgwi Writing Trainer/Collection Editor
Prof Salisu Yakasai and Prof Lawan D Yalwa Hausa Language Consultants
Nas Yakubu Bloom Trainer
Story Writers Husaini Adamu; Adamu Babbikoi; Garba Mohammed Dantsoho; Jalauddeen Ibrahim Maradun; Yasalu Haruna; Muhammed Umar Deba; Idris Hamid; Ibrahim Baraya; Dahiru A Yelwa; Mansur Isah Buhari; Grace Malgwi
Illustration from International Illustration:The Art of Reading 3.0 Copyright:  SIL International 2009



Al'ada madubi ce ta rayuwar Al'umma.
Kowacce al'umma tana da al'adarta.
Al'ada ta danganci yadda al'umma ke al'amuransu.
Kuma tana yaɗuwa tsakanin al'umma.

Al'adun jama'a sun ƙunshi abubuwa da yawa.
Yadda al'umma ke magana al'adda ce.
Yadda suke sa kaya al'ada ce.
Yadda suke yin biki ma al'adda ce.
Yadda suke dafe-dafensu ma al'adda ce.












Al'ada ta bambanta a tsakanin al'umma.
Al'adar Hausawa ta bambanta da ta Bafulatani.
Al'adar Yarbawa ta bambanta da ta Hausawa.
Al'adar Inyamuri ta bambanta da ta Yarbawa.

Al'addar kowace al'umma ta kasu kashi biyu.
Akwai al'ada da ake gani kuma a taɓa.
Misali kamar sutura da gidaje.
Akwai kuma dafe-dafe da kayan abinci.











Kashin al'adar na biyu sune wadanda ba'a gani.
Misali shi ne yadda ƙabilar ke magana.
Akwai  kuma yadda take gaisuwarta.

Al'ada tana taimakawa kabila wajen sanin tarihinta.
Al'ada na haɗa kan al'umma.



ALL CHILDREN READING: A GRAND CHALLENGE FOR DEVELOPMENT
USAID FROM THE AMERICAN PEOPLE
World Vision
Australian Aid
GLOBAL READING NETWORK